# Littafi mai Tsarki na yara

**Ke gabatar da**



# Kyakkyawar Sarauniya Esta

**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Janie Forest**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Ruth Klassen**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan**
**har ba zaku sayar da shi.**

**An taba yin wata kyakkyawar yarinya mai suna Esta. Bayan da babanta da mamanta suka mutu, dan’uwanta na dangi wani mai suna Modekai ne ya rayar da ite. Esta ta daukaka dn’uwarta ta wurin yin masa biyayya a matsayin ‘yar mai kirki.**





**Esta ta yi zama a Farsiya.  Amma, it ba ‘yar Farsiya ba ce.  Ita Bayahudiya ce.  Kakkaninta sun zo Farsiya bayan da aka kwashe su bayan an ci su da yaki.  A kwanakin Esta, akwai Yahudawa da yawa da suke zama a Farsiya.**

**Sarkin Farsiya ya yi wani babban biki wa sarakuna daga ko’ina a duniya.**



**Mazan suka ci abinci daban da matan da su ma suna nasu bikin tare da Sarauniya Vashti. Sai Sarki cikin jiri ya ba da umarni ga Sarauniya Vashti ta saka Rawanin Saraauta don ta nuna kyanta. Sarauniya Vashti ta ki.**

**Donya nuna cewa yakamata mata su daukaka mazansu, sarki ya ba da doka wanda ya kwace rawanin daga Vashti.  Ya nuna ita ba sarauniya kuma ba.**



**Sai aka fara neman sabuwar sarauniya. Daga cikin duka kyawawan ‘yan matan birnin, sai sarki ya zabi Esta ta zama matarsa. Sai ya saka rawanin sarauniyar a kanta. Esta ba ta gaya wa sarki cewa ita Bayahudiya ba ce saboda dan’uwanta ya gaya mata kada ta fada.**



**Dan’uwanta Modekai ya tsaya a bakin kofar shiga gidan sarki domin ya ji labari game da Esta.**



**Wata rana sai ya ji wadansu ‘yan hidima guda biyu a gidan sarki suna shiri su kashe sarki. Modekai ya ba da shawara wanda ya cece ran sarki. ‘Yan hidimar aka kashe su ta wurin rataya, sai sunan Modekai ya shiga cikin sunayen takardar sarki.**

**Mabiye da sarki shi ne wani mai arziki mai suna Haman. Kowa yana sujada yayinda da Haman yana wucewa. Kowa da kowa – ban da wani mutum daya. A matsayinsa na Bayahude, Modekai yana sujada wa Allah mai rai ne kadai.**



**Haman ya ki jinin Modekai sosai sai ya yi shiri ya kashe shi da duka Yahudawan da suke a Farsiya. Abin mamaki! Sai Haman mai mugunta ya yi wa sarki wayo domin ya fitar da wani doka cewa a shiryayen lokaci za a kakkashe duka Yahudawa a mulkin.**





**Wannan mummunar doka ne. Da Yahudawa da Farsiyawa, duka suka yi makoki. Amma tuna – Allah ya riga ya mai da Esta Sarauniya. Kuma ita Bayahudiya ce. Za ta iya boye asirinta ga sarki? Ko kuma, za da dauki hatsarin mutuwa don ta cece mutanenta?**

**Allah ya ba wa Esta wani tunani mai kyau.  Sai ta gayace sarki da Haman ga biki.  A wurin sarki ya yi mata alkawari cewa zai ba taduk abin da ta roka.  “Bari sarki da Haman su zo bikin… gobe,” Esta ta amsa.  Sa’an nan ne za ta gaya wa sarki abin da take so.**



**Tukuna dai, Haman ya riga ya shirya kato wurin rataya mutane inda zai rataye Modekai don ya mutu.**



A daren nan sarki bai iya barci ba. Da ya karanta tarihin gidansa sai ya ga cewa ba a taba ba wa Modekai lada don ya ceceransa ba. Washegari, sai ya sarki ya tambaye Haman, “Mene za a iya yi wa wani wanda sarki yana jin dadinsa



domin a girmama shi?” Haman ya ji dadi. Yana gani kamar shi ne sarki yake nufi!



**Haman ya riga ya zo on ya nemi iznin sarki don ya rataye Modekai. Wurin ratayen yana a shirye. Yanzu sai wurin ya jira kadan. Cikin farin ciki, Haman ya zubo da shawarwarensa da ra’ayinsa. “A yi wa mutumin sutura da rigunan sarki da rawani.”**

**"A sa ya zauna a kan dokin sarki. A umarta dan sarki ya bi da mutumin a cikin titunan birnin domin kowa ya gani." "Yi sauri, je ka yi haka wa Modekai Bayahude," sarki ya umarta Haman.**



Aganinka yaya ne Haman ya ji yayinda yake bi da Modakai cikin daukaka kewaye da birnin? Ya ki jinin Modekai fiye da da. “Dakata,” watakila Haman ya dan yi tunani. “Ba da daddewa ba zai mutu – tare da saura Yahudawan.”



Can an jima a ranar, Haman da sarkin suka kai wurin bikin Sarauniya Esta. “Mene ne kararka?” sarki ya tambaya. Bai manta da alkawarinsa ba. Mika hannu a kan Haman, Sarauniya Esta ta fada wa sarki kome da kome game da mugun kulle-kullen Haman. ‘A rataya shi!’ sarki ya ce.



**Sai sarki ya ba da wani doka wanda ya bar Yahudawa su tsare kansu. Aka cece su! Modekai ya zama mabiye da sarki kuma duka Yahudawa suka yi farin ciki suka ba daa kyautayi wa juna. Har wa yau, Yahudawa suna tuna yadda Allah ya cece su ta wurin kyakyawar Sarauniya Esta.**



# Kyakkyawar Sarauniya Esta

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**Esta**

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**

# KARSHE

30

60

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**